# Littafi mai Tsarki na yara
## Ke gabatar da

# Nuhu da Ruwan Ɗufana




Wanda ya Rubuta: Edward Hughes

Mai Zane: Byron Unger; Lazarus
Alastair Paterson

Fassarawa: Maren Dameng Daniel

Mai niyyan daukan nauyi: M. Maillot; Tammy S.


Labari na daya 3 daga cikin sittin 60


**www.M1914.org**

***Bible for Children,*** *PO Box 3, Winnipeg, MB R3C 2G1 Canada*



Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.


Hausa



**Nuhu mutumi ne mai bauta wa Allah da sujada. Dukkannin sauran jama'a sun tsane shi kuma basu yin biyaya ga Allah. Wata rana Allah ya yi magani mai ban mamaki. “Zan halaka duk mugayen mutane da duniya nan,” Allah ya gaya wa nuhu. “Iyalen ka ne kaɗai za su tsira.”**





**Allah ya faɗawa Nuhu zai aiko da ruwa wanda zai rufe duka duniya. “Ka sassaƙa baban jirgi wanda zai lya ɗaukan lyalan ka da kuma dabobi masu yawa ,” Allah ya umurci Nuhu. Allah ya faɗawa Nuhu yadda zai sassaƙa jirgin. Sai Nuhu ya fara!**


Mutane kuwa sun yi wa
Nuhu ba'a yayin da ya
gaya masu dalilin sa na
sassaƙa jirgin. Nuhu
kuwa ya
ci guba da
aikin sa.
Kuma yana
yaɗa bishara
yana wa'azi akan
Allah. Amma ba
wanda ya ji shi.
3


Nuhu kuwa ya bada gaskiya
mai yawa. Ya yadda da
Allah duk da ruwan sama
bai taɓa sauƙa. Bada bata
lokaci ba jirgin ya kammala
domin ɗaukan kaya.
4


Sai dabbobi suka zo. Allah ya kawo ire-ren dabbobi guda
baƙwai, da biyu na sauran. Tsuntsaye manya da kanana,
dabbobi ma kanana da dogaye suka kama hanya
zuwa cikin jirgin.
5


Kodayake mutane sunyi ta ihu
suna zagin Nuhu ya yin da yake
shigar da dabbobi cikin jirgin.
Basu daina zunubi wa Allah
ba. Basu kuma nemi
izinin shiga jirjin ba.
6


A ƙarshe dukan
dabbobi da
tsuntsaye sun
shiga cikin
jirgin "shigo
cikn jirgin" Allah
ya gayyaci Nuhu
"kai da iyalen ka." Nuhu,
da matarsa, yaran sa uku
da matansu suka shiga jirgin.
Sai Allah ya rufe kofan jirgin!
7


Sai ruwan sama
ya sauƙo. Wannan ruwan
mai yawan gaske da aka yi ya
jika duniya na tsawon
kwana arba'in.
8


Ruwan ɗufanan ya watsu zuwa birane da kauyuka. Da ruwan ya tsaya, dukan tsaunuka sun shiga cikin ruwa. Kowane abu da yake numfashi sun mutu.
9
Lokacin da ruwan ɗufana ya cika duniya, sai jirgin yayi ta tafiya a saman ruwan. Zai iya kasan cewa da duhu ko gargada ko abu tsoro. Amma jirgin ya tsare nuhu daga ruwan ɗufana.
10
Bayan wattanni biyar na ruwan ɗufana, sai Allah ya aiko da iskar guguwa mai bushar kasa. A hankali jirgin ya sauko daga tudun Ararat. Nuhu ya kasance cikin jirgin na tsawo kwana arba'in da yini arba'in yayin da rowan ya tsaya.
11
Nuhu ya fitar da hankaka da kurciya ta taga. Basu sami wurin da za su huta mai tsabta ba, sai kurciya ta dawo wurin Nuhu.
12
Nuhu ya fitar da hankaka da kurciya ta taga. Basu sami wurin da za su huta mai tsabta ba, sai kurciya ta dawo wurin Nuhu. Bayan mako daya sai Nuhu ya sake fitar da kurciya. Kurciyar ta dawo da ganyen zaitun a bankita. Bayan wata makon Nuhu ya gane cewan duniya ta bushe domin kurciyar bata dawo ba.
13
Ubangiji ya fada ma Nuhu cewan lokaci yayi da zaku fita daga wannan jirgin. Nuhu tare da iyalensa suka fitar da dukkan dabbobin daga cikin jirgin.
14










**Nuhu da Ruwan Ɗufana**

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

Farawa 6-10

“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130

Allah ya san da cewa munyi abubuwan da basu da kyau, wanda a ƙira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne.

Allah yana kaunan mu sosai Ya kuma aiko da ɗansa, Yesu, domin ya mutu a kan giciye, kuma ya biya sakamakon zunuban mu. Yesu ya tashi kuma ya koma sama! Yanzu Allah zai yafe mana zunuban mu.

Idan kana so ka juyo daga zunuban ka, ka faɗawa Allah wannan: Ya Allah, na bada gaskiya ga Yesu ya mutu domina kuma yanzu ya na yare. Ina rokon ka, ka shigo cikin zuciyana kuma ka yafe min zunubai na domin na samu sabon rai kuma na zauna da kai har abada. Ka taimakeni in yi rayuwa da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amen. Yahaya 3:16

Ka karanta littafi mai-tsarki ka kuma yi Magana da Allah a kulla yamin!